LUMBU-LUMBU

(Wutar Ƙaiƙayi)

LABARI/RUBUTAWA

KHADIJA S.SAMINU

(YʻAR GATAN MAMA)

Gajeren Labari

SHAFI NA FARKO DA ƘARSHE.

****

Dattijuwar mace ce a zaune akan sallaya hannunta ɗauke da carbi tana ja taji ana rafka sallama a ƙofar gidan,amsawa ta shiga yi ba ƙaƙƙautawa amma hakan bai hana mai sallamar cigaba dayi ba har ta fara tunanin kodai kurma ne wanda hakan ya tilasta mata ta tashi ta leƙa don ganin wake magana haka.

"A'a! Malam Habu kaine haka kake sallama kamar baƙo?"

Ta faɗi haka ga baƙon da yake sallamar,gyara tsayuwarsa yai tare haɗe hannuwansa ya rungume sannan yace da ita...

"Ni ne Hajiya Hauwa,nayi sallamar ne saboda cika umarnin Manzo sallallahu alaihi wasallama da yake cewa: 'Idan ɗayanku ya nemi izini sau uku,ba'a amsa masa ba,to ya tafi'. Wannan dalili yasa kika ga na tsaya anan saboda ni ba muharraminki bane ba,ni ɗan uwan mijinki ne da yabar duniya yabarmin amanar ke da ɗanki,kuma Allah ya gani ina iya ƙoƙarina wajan ganin na riƙe wannan amanar da ya barmini,sai dai me?, wannan ɗannaki *ALIYU* Allah ya zubamasa rashin ji kamar jinjirin jaki sam baya ɗaukar nasihar da ake mas..."

"Innalillahi wa'inna ilaihi raji'un! Malam dan Allah ka sanar dani me yaronnan yaje yayi haka,wallahi jikina duk rawa yake na gaji da kawo ƙarar ɗannan da akemin Malam.!"

Ta katseshi da faɗin haka tare da jan gefen hijabinta ta fara goge hawayen fuskarta.Kallonta tare da fara mata bayanin abinda Aliyun yai kamar haka...

"Kinga Hauwa tsaya kidena kukanga haka a ƙwar gida wani ya aza bugunki nai a wanga wuri haka bamai fiddani sai Allah."

Sharce majinar hancinta tayi tare da cewa."Ina jinka Malam."

Shima gyara tsayuwarsa yai sannan yace...

"Ai nasan kina da labarin *ALHAJI ISHAƘ ZAKI*,wanda ke neman takarar gwamnan jihar nan tamu,to shi ne yai musu alƙawarin wasu manyan kuɗaɗe tare da sa su aikin sara suka gaduk wanda yace bazai zaɓeshi ba,kuma cikin ikon Allah sun samu nasarar illata mutane da dama ta hanyar ji musu raunuka,sannan sunyiwa masu kantina ɓarna ta hanyar shiga suyi musu watsi da kayan sana'arsu wanda dalilin hakan sukari ya haɗe da gishiri,madara ta haɗe da garin fulawa,sannan kuma ile an saci yara huɗu a daren jiya wanda ake kyautata zaton yɑn ƙungiyar su Aliyunki ne dan yanzu hakama sunacan ofishin yɑn sanda ana gudanar da binkice."

Hajiya Hauwa ɗora hannu tai aka tare da jingina da bango tahau faɗin...

"Innalillahi wa'inna ilaihi raji'un!" kafin ta sauke wata ta kama wata.Nan suka tafi da Malam Habu dan suji inda maganar ta ke yanzu,ko da sukaje ba wanda ya sauraresu yɑn sandan sunce bazasui magana da kowa ba sai sun gama bincike.

Tsawon mako huɗu su Aliyu suna ɗaure ana yi musu horo mai tsananin gaske wanda duk seda jikkunansu sukai sanyi,basui nadama tare da shiga tashin hankali ba har sai randa Alhaji Ishaƙ zaki yazo amsa tambayoyi,gabaki ɗayansu tunaninsu komai yazo ƙarshe dan haka suka fara kumbure-kumburen fuska.

Alhaji Ishaƙ Zaki ne ya kallesu baki ɗayansu yana ƙara kallonsu kamar yau ya taɓa ganinsu,memakon ya amsa tambayar da hukuma tai masa saima tashi da yai tsaye ya hau bambamin bala'i...

"Haba Officer,ya ya zaka gayyatoni irin wannan wajan dan naga yaran da ko kusa basu da tarbiyya?,ni mahaukaci ne da zan tara yan jagaliya a matsayin mutanen da zasu zaɓe ni ko zasu sa a zaɓe ni,ai tafiya irin wannan masu ilimi da sanin ya kamata ake samu waɗanda zasu amfani kansu da al'umma ba irin waɗannan da iyayensu ma kuka suke dasu ba.Dan Allah kar a ƙara ɓatamin lokaci akan irin waɗannan abubuwan marasa ma'ana."

Yana zuwa nan a zancensa yai ficewarsa yayin da wasu daga yan sandan suke rakashi da addu'a inda wasu kuma suka bishi su rakashi har bakin motarsa.

Jikinsu ne yai sanyi yayin da lokaci ɗaya sukaji wata iriyar nadama ta baibaye su,kasancewar case ɗin na manya ne ta ke aka rufe babinsa aka sanya wasu kuɗaɗe masu nauyi a matsayin kuɗin belin su Aliyu.Jin haka yasa Malam Habu tattaki ya je ya sanarwa Babar Aliyu,hankalinta ya tashi da jin yawan kuɗin amma ba yadda ta iya haka ta ɗaga kayan ɗakinta da yan kadarorinta ta saida taje belin nasa.

Shigarta Police station ɗin ke da wuya se ga babar aminin Aliyun itama ɗan uwansa ya ruƙo hannunta sunzo suma su fanshe shi,bayan anyi duka cuku-cukun da za'ai ne aka basu yaransu tare da kashedin gaba idan aka kuma kama su da wani laifin makamancin wannan sedai su ƙare rayuwarsu a gidan *ƊAN KANDE*.

Fitowarsu harabar ofishin ke da wuya Aliyu ya kalli yayan aminin nasa me suna Ya'aƙub tare da ƙasa da muryarsa yace masa...

"Ɗan uwa ka temakeni ka tayani bawa Umma haƙur.."

"Da..da banyi haƙurinba ina zan waiwaye ka,da mutuncinka da komai kaje kana son illata rayuwarka ta hanyar sanya kanka cikin yan *BANGAR SIYASA*, wallahi tallahi Ali..."

Umman Aliyu ke wannan maganar yayin da ta iso nan se sukaji ɗif kamar ɗaukewar ruwan sama tayi tsit kafin sui wani tunani ta faɗi a wajan,kuka Aliyu ya shiga yi cikin matsanancin tashin hankali,hanzarin samun abun hawa sukai suka tafi asibiti da ita ko kafin su je Allah ya ɗauki rayuwarta.

Tunda wannan abu ya faru Aliyu ya rame ya ƙanjame ya fita daga hayyacinsa,bashi da aiki ko yaushe sedai idan ya tara yara masu tasowa yaita musu nasiha da idan sun girma kada su yarda su shiga *BANGAR SIYASA*,Kar su yadda wani ya basu kuɗi ya haɗa kai dasu su rusa ƙasarsu da al'ummarsu,bangar siyasa ba tasu bace,duk wanda yai musu tayi suce yaje ya bawa ɗansa yai masa aikin ko ya haɗashi da ɗansa sui aikin ta'addancin,indai har yaƙi yadda to suma kada su yarda domin kuea duk abinda zaiyi musu ba kamai bane illa *LUMBU-LUMBU(Wutar ƙaiƙayi)*. Shima sanadin haka ya rasa mahaifiyarsa ya dawo maraya ba Uwa ba Uba,kuma har ya koma ga Ubangiji bazai dena kukan rashinta ba,dan koyaushe gani yake kamar shi ne ya kashe tunda silar baƙin cikin da ya sata ne ta mutu.

Haka kuma abokansa duka sun shiryu sun tsaya sunyi aikin ƙarfi domin su samu na sanyawa a bakin salati da kuma wanda zasu kai gida na sa albarka,shi kwa Aliyu da ke yanzu ya zama maraya idan yai faskaren ice sai dai ya kaiwa ƙanin mahaifinsa Habu yaiwa iyayensa sadaƙa,sauran yaci abinci ya tallafawa na ƙasa dashi saboda yana gudun rashin kuɗi suma ya jefasu a *BANGAR SIYASA*,dan shi dalilin rashin tsayayyiyar sana'a da ɗaukar nauyin Mahaifiyarsa su suka taka muhimmiyar rawa wajan afkawarshi *BANGAR SIYASA*,yanzu ya gane shiyasa yake yaƙi da zaman majalisa da gulma ya kama sana'a.

Alhamdu Lillah.